# KUNDIN SAMAR DA TSARIN CI GABAN GARIN KADEMI

*Tsarawar*

**Cibiyar Bunƙasa Fasahar Sadarwa Da Ci Gaban Al'umma (CITAD)**
**Tare Da**
**Gudummawar Ƙungiyar ActionAid Ta Najeriya (AAN)**





## ABUBUWAN DA KE CIKI

Shafin Farko....................i
Jadawali....................ii
Godiya....................1
Gabatarwa....................2
Manufa....................3/4
Hanyoyin Da Aka Yi Amfani Da Su....................5
Tsarin Da Aka Yi Amfani Da Shi....................5
Cikakken Bayani Game Da Garin Kademi....................5/6
Tarihin Garin Kademi....................6/9
Taswirar Garin Kademi....................9/10
Yanayin Zamantakewa....................11
Lafiya....................11
Ilimi....................12/14
Juyawar Yanayin....................15
Kadarori....................16
Tantance Matsalolin Da Ke Addabar Garin Kademi....................17/18
Tantance Haƙƙoƙin Mata....................19/21
Take Haƙƙoƙin Ɗan Adam....................22/24
Kalubalen Da Ke Fuskantar Garin Kademi A Halin Yanzu....................25/28
Tantance Matsaloli Ta Amfani Da Bishiyar Matsaloli....................29/30
Tantance Yanayin Karfin Iko (Nazari Kan Waɗanda Keda iko)....................31
Tantance Hanyoyin Samun Bayanai....................32/33

Wani mutum wanda ake kira Malam Kadai (Kanuri) shi ya samar da garin, mutumin yazo ne daga jihar Barno. Bayan shekaru da dama garin ya samu haɓakar jama'a masu yawa wanda yasa jama'ar garin suka yanke shawarar samun matsuguni na dundundun. Wannan yasa suka koma inda garin Kademi yake a yanzu inda suka share dajin dake gurin suka kuma shuka bishiyoyi da samar da gonaki domin noma. Daga nan ne ake yiwa wannan guri laƙabi da ƙauyen Malam Kadai, haka garin ya cigaba da haɓaka har zuwa yadda yake a yanzu.

Malam-Kadai shi yayi addu'ar Allah yakare garin daga rushewa ta hanyar yaƙi ko yunwa ko kuma sanadiyar annoba da wasu masifun. An taɓa samun iftila'i na gobara a gabaɗayan garin wadda ta haifar da hasarar rayukan jama'a, yayinda sauran jama'ar da gobarar bata shafa basuka tashi suka bar garin. Sun zauna a wannan gari sama da shekara ɗari (100). Bayan nan ne Malam Kalu da jama'arsa suka zo suka zauna a wannan gari. Duk da yake Malam Kalu ya sami labarin Malam Kadai mazaunin garin na farko, ta haka ne garin ya samo sunansa na Kademi.

Jerin Hakiman da suka taɓa jagorantar garin

| | SUNA | DAGA | ZUWA |
|---|---|---|---|
| 1. | MalamKadai | 1788 | 1804 |
| 2. | MalamKalu | 1804 | 1831 |
| 3. | Dundumajo | 1831 | 1848 |
| 4. | Mohammadu I | 1848 | 1878 |
| 5. | Mohammadu II | 1878 | 1879 |
| 6. | SarkiDabo | 1879 | 1900 |
| 7. | SarkiSambo | 1900 | 1928 |

Waɗannan su ne jeran sunayen da suka mulki garin a ƙarƙashin mulkin Kanuri. Waɗanda suka mulki garin a ƙarƙashin mulkin Fulani kuwa sun haɗa da:

| | SUNA | DAGA | ZUWA |
|---|---|---|---|
| 1. | Sarki Sa'idu | 1928 | 1940 |
| 2. | Adamu Sa'idu | 1940 | 1944 |
| 3. | Mal. GiɗaɗoAbdullahi | 1944 | 1948 |
| 4. | Alh. Yakubu | 1948 | 1963 |
| 5. | Alh. Sule | 1963 | |





SANA'OI /AIKIN YI:

Dangane da sana'o'i da ayyukan yi kuwa, sama da kaso 70 na mazauna wannan gari na Kademi Manoma ne. suna noma abin da zasu cida kuma wanda zasu sayar. Abubuwan da suke nomawa domin ci sun haɗa da Gero, Dawa da kuma Rogo. Haka nan abubuwan da suke nomawa domin siyarwa sun haɗa da Wake da Gyaɗa. Da dama daga cikin mazauna wannan gari makiyaya ne, inda suke kiwon Shanu da Tumaki.Tsiraru daga cikin mazauna garin kuma ma'aikatan gwamnati ne.

ABUBUWAN MORE RAYUWA: -

Garin Kademi na da ruwan sha sai dai ba ko yaushe ake samun ruwan ba, saboda wani lokacin akan ɗauki kwanaki goma sha biyar a wata ba tare da an sami ruwanba. Wannan dalilin ne yasa mutane ke amfani da rijiyoyi da fanfan tuƙa-tuƙa wajen samun ruwan sha. Hakan nan ba a fiye samun wutar lantarki ko da yaushe a garin ba.

ILIMI: -

Dangane da ilimi kuwa, akwai masu ilimin addini da na zamani da yawa a garin Kademi. Akwai makarantun firamare guda 3 da makarantar sikandire 3 a garin.


LAFIYA

Akwai ɗakin shan magani wanda al'ummar wannan gari ke amfani da shi dangane da matsalolin da suka shafi lafiyarsu da kuma ɗigon maganin shan inna (NPI). Haka kuma akwai ɗakin shan magani da aka tanada domin kula da lafiyar dabbobi a garin. Tazarar kilomita 0.5 tsakanin ɗakin shan maganin daga cikin garin. Ɗakin shan maganin nada ƙwararrun ma'aikatan lafiya 11, 8 daga ciki maza ne 3 kuma mata. Koyaushe akan sami ma'aikatan lafiyar a wannan wuri kamar yadda mutanen Kademi suka zayyana. Idan kuma aka sami ɓarkewar cututtuka sukan sanar da hukumar da abin ya shafa ta hannun Dagacin garin dasauran jami'an lafiyar. Waɗanda cututtuka suka fi yiwa barazana su ne ƙananan yara 'yan ƙasa da shekaru 5.Mutanen wannan gari sun bayyana cewa matakan haihu a gida a mafi yawan lokaci wani lokacin kuma wasu matan tsiraru kan haihu a ɗakunan shan maganin garin.

Idan haihuwa tazo da tangarɗa akan kai mata asibitin Gaya su haihu a can duk da yake dai an ɗan sami cigaba shekaru 3 da suka wuce, wani lokacin ma akan bada magunguna kyauta a ɗakunan shan maganin.

## TASWIRAR GARIN KADEMI

Samar da taswirar ya soma ne da tattaki cikin ƙwaryar garin.Al`umar yankin ne suka gudanar da tattakin wajen zana tasawirar yankin nasu, inda suka nuna mahimman wurare da albarkatun da suke dasu da kuma ƙalubalen dake fuskantar a yankin da ababan more rayuwa da abubuwan dake musu barazana.An tattauna mai zurfi don sanin haƙiƙanin garin a ƙoƙarin samar da taswirar, yayin da aka bayyana albarkatun ƙasa da abubuwan more rayuwa da sauran arziƙin da Allah ya horewa garin. Albarkatun ƙasar da Allah ya horewa garin sun haɗa da koguna masu dama wanda kogin Dudduru shi ne kogi mafi girma da yafi kusa da garin. Ga kuma albarkar ƙasar nomada kiwo.




Taswirar Garin Kademi







Figure i: Matan Garinwajen Samar da Taswirar Yankin.



Figure ii: Hanyar da ruwa ke ambaliya tsakanin garin Kademi da Wudilawa

# KALUBALE

## Kalubalen Da Ke Fuskantar Garin Kademi A Halin Yanzu

Garin Kademi ƙauye ne da shekaru da dama ke fuskantar matsaloli masu yawa. Matsalar hanya itace matsalar da tafi damun mutanen wannan garin a duk cikin matsalolin, banda wannan matsalar ta hanya da gadoji, wannan garin na buƙatar kayayyakin aiki a asibitocinsu da jami'an lafiya, sannan da ƙarin makarantu da tsabtaceccen ruwan sha.


An jera matsalolin wannan garin ta hanyar tsarin na matsalar da tafi ciwa al'umma tuwo a ƙwarya a sama. Jama'ar wannan garin sun zaɓi matsalar hanyar mota da rashin wadatattun gadoji da rashin makarantu su kasance manyan matsalolin garin. Magance waɗannan matsalolin zai taimaka sosai wajen magance sauran matsalolin wanda suka haɗa harda matsalar rashin aikin yi. An sanya matsalar gada ta zama babbar matsala ta biyu da tafi damunsu , yadda idan aka magance matsalar zata rage taɓarɓarewar ayyukan kasuwanci a yankin ta kuma haɓaka daukar yara a makarantu da riƙesu ta kuma rage matsalar mutuwar mata masu juna biyu gurin haihuwa da sauran matsalolin da suka danganci lafiya ga jama'ar wannan gari. Hakan zai kawo sauƙin zirga-zirga tsakanin wannan garin da sauran maƙotanƙauyika da ke zagaye da wannan garin tare da bunƙasa hanyoyin sadarwa a tsakanin garuruwan.

## SASSAUKAR HANYAR JERA MATSALOLI

| Al'amari | MATA | YARA | MAZA | ADADI | MATSAYI |
|---|---|---|---|---|---|
| Rashin aiki | 27 | 53 | 29 | 100 | 1ST |
| Ilimi | 21 | 16 | 25 | 62 | 2ND |
| Wutar lantarki | 31 | 32 | 9 | 72 | 3RD |
| Rashin ruwan sha | 17 | 05 | 0 | 22 | 4TH |
| Asibiti | 13 | 11 | 17 | 41 | 5TH |
| Hanya | 02 | 18 | 22 | 42 | 6TH |
| Shan miyagun ƙwayoyi | 02 | 02 | 01 | 05 | 7TH |








Jeran Matsalolin Jama'ar Kademi



**Figure vi: Mata da** ƙananan yara ke ɗeban ruwa a rijiyar Gandu a firamaren garin Kademi

